# Yadda Za Ka Zaɓi Wanda Za Ka Bi Misalinsa

Wanne za ka fara zaɓa, halin da kake so koya ne ko kuma mutumin da kansa? Duka biyun za su iya taimakawa.

## ZABI NA A

**Ka zaɓi halin da kake so ka koya, kuma ka nemi mutumin da yake da wannan halin.**

***Wata mai suna Alana ta ce: "Abin da ya taimaka min in sami wanda zan koyi halinsa shi ne, sanin asalin halin da nake so in koya, sa'an nan in nemi wanda yake da irin halin."***



## 1 KA SAN HALIN

**Ka'idar Littafi Mai Tsarki:**

"Guduna ba na banza ba ne."—1 Korintiyawa 9:26, *Juyi Mai Fitar da Ma'ana*.

Wane hali ne kake so ka koya?

..............................................................

## 2 KA ZAƁI MUTUMIN

**Ka'idar Littafi Mai Tsarki:**

"Ku zama masu koyi da waɗanda ke gāda alkawarai ta wurin bangaskiya da haƙuri." —Ibraniyawa 6:12.

**Ka zaɓi tsararka, ko wani da ya manyanta, ko kuma wani daga Littafi Mai Tsarki da ya nuna halin da ka zaɓa da farko.**



1. Tsararka

..............................................................



2. Wanda ya manyanta

..............................................................



3. Wani daga Littafi Mai Tsarki

..............................................................



www.jw.org © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

# ZAƁI NA B

Ka zaɓi wani da kake so, sai ka ambata halin da shi ko ita ta nuna da ya burge ka.

*Wani mai suna Colin ya ce: “Abokina yakan tsara yadda yake kashe kuɗinsa kuma ba ya sayan abubuwa barkatai, hakan ya burge ni kuma na bi misalinsa.”*

## 1 KA ZAƁI MUTUMIN

Ka rubuta sunayen mutanen da kake so ka bi misalinsu. Kana iya rubuta sunan, tsararka, ko wani da ya manyanta, ko wani daga Littafi Mai Tsarki.



## 2 KA SAN HALIN

Bayan haka, sai ka rubuta halin da kake so da kowannensu yake da shi.

| Mutumin | Halin |
|---|---|
| | |
| | |
| | |
| | |
| | |

Ko A ko B ne ka zaɓa, mataki na 3 ɗaya ne



www.jw.org © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

# 3 KA YI TUNANI, SA'AN NAN KA YI KOYI DA HALIN

## Ka'idar Littafi Mai Tsarki:

"Ku dubi ƙarshensu, ku kuma yi koyi da bangaskiyarsu."—Ibraniyawa 13:7, *Littafi Mai Tsarki.*

Me ya taimaka wa wanda nake so in bi misalinsa ya kasance da halin da nake so in koya?

Waɗanne tambayoyi ne zan yi ma wanda nake so in bi misalinsa?

## Ka Lura:

Idan kana so ka yi koyi da wani da ke cikin Littafi Mai Tsarki, tambayar da kake so ka yi masa ne za ka yi amfani da shi wajen yin binciken ka.

Mene ne zan yi wannan makon don in yi koyi da mutumin da na zaɓa?

## Taimako

Ka mai da hankali ga yadda za ka koya *halin* maimakon gwada abin da ka cim ma da wanda mutumin ya *yi.*
—Galatiyawa 6:4.





www.jw.org © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania